# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Sarki Solomon Mai Hikima

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

**Sarki Dawuda babban mutumin Allah ne. A lokacin mulkinsa Isra'ila ta yi girma har sau goma fiye da da a lokacin Sarki Shawulu. Amma yanzu bai iya mulki ba.**



**Dawuda ya tsufa. Kuma ya gaji! Kuma ga ciwo! Rayuwarsa a duniya yana zuwa ga karshe.**

**Daya daga ‘ya’yan Dawuda masu yawa,**



**Adonija, ya gaya wa mutanen Isra’ila cewa yanzu shi ne zai zama sarki. Ko da yake ma’anan sunan shi shine “Ubangijina ne Allahna”, Adonija ba mutumin kirki ba ne. Ya yi kokarin yadda zai sata kursiyin, kuma ya sani Dawuda ba shi da karfin da zai dakatar da shi. Amma Allah yana da wadansu shirye-shirye!**

**Matan Dawuda Betsheba ta sani dan ta Solomon shi ne yakamata ya zama sarki.  Sai ta gaya wa Dawuda shirin Adonija. Duk da ciwonsa, Dawuda ya tattara shugabannin tare a gaban jama’a sai ya mai da Solomon sarkin Isra’ila.**



**Solomon ba shi da matsalla da Adonija saboda mutanen Isra’ila sun amince da Dawuda. Dawuda ya fada musu Solomon shi ne wanda Allah ya zaba ya zama sarkinsu. Ba a dadde ba sai Dawuda ya mutu.**





**Kafin Dawuda ya mutu, ya yi magana da Solomon game da yin biyayya ga Allah da kuma zama sarki mai kyau. “Ka yi tafiya a hanyoyin Allah, domin ka yi nasara a cikin dukan ayyukanka,” Dawuda ya gaya wa dansa. Wannan shawara mai kyau ne!  Sa’an nan Solomon ya zauna a kursiyin mulkin babansa, Dawuda, kuma mulkinsa ya kafu daram.**

**Wata rana da daddare,
Solomom ya yi mafarki.
A mafarkinsa, Allah ya
bayyana gareshi ya
ce, “Roka!  Mene
ne zan ba ka?”
Da kai ne da
mene ne za
ka roka?**



**Solomon ya roka a ba shi hikima domin ya zama sarki mai kyau. Roko na Dan saurayi sarkin ya faranta wa Allah rai. Allah ya ba shi abin da ya roka – amma ya kuma yi masa alkawarin arziki da girma.**





**Ba a dadde ba da mutane suka gane hikimar Solomon. Wata rana, mata biyu suka zo wurinsa, da 'yar jariri daya. "Maccen nan, yaronta ya mutu da daddare, sai ta dauki mataccen ta ajiye mini," dayan ta ce. "A'a! Amma yaro mai rai din YARO NA ne, matacen shi ne naki." dayan ta ce. Yaya ne sarki zai sani ko wane ne uwar da gaske?**

Sai sarkin ya ce, “Ku kawo mini takobi.”  Sai suka kawo takobi a gaban sarki.  A ganinka mene ne sarki yake shirin yi da takobin?



**Sai sarki ya ce, "Raba yaro mai rai din kashi biyu sai a ba kowa rabi." Sai uwar yaro mai rai din ta ce, "Ya mai gida, ka ba ta yaro mai rai din kuma ko ta yaya kada ka kashe shi."**



**Amma dayan ta ce, “Bari kada ya zama nawa ko naki, amma a raba shi.”**





**Sai sarki ya ce, "Ku ba wa mace ta farkon yaro mai rai din. Ita ce uwar." Kuma duka Isra'ila suka ji shari'ar, kuma suka girmama sarkin sosai. Suka gani cewa hikimar Allah tana a cikinsa.**

**Mutanen Isra'ila ba su da haikali inda za su yi wa Allah sujada. Sa'ad da Dawuda ya so ya gina wani, sai Allah ya ce masa. "Danka zai gina gidan domin SUNANA." Ta haka Solomon ya fara gina haikali mai kyau a Urushalima.**



Ya dauki shekaru masu tsawo bakwai kafin a gina haikalin. Amma babban ranar ta kai wanda kowa ya taru domin a ji Solomon yana mika haikalin ga UBANGIJI.



**Bayan addu'a mai muhimminci, sarki da mutane cikin farin ciki suka mika hadayu dubbun dubbai suka kuma yi**



**babban biki na makoni biyu.**

**Bayan wannan, Allah ya sake bayyana kansa ga Solomom ya yi masa alkawari zai albarkace shi da Isra’ila muddin suna yi masa biyayya.**





Abin bakin ciki, da Solomon da mutanen Isra’ila, babu wanda ya yi wa Allah biyayya. Sarkin ya auri mata da yawa wadanda Allah bai so ya aura ba. Matansa masu taurin kai suka juya masa zuciya zuwa bautan gumaka; zuciyarsa kuma ba ya biyayya ga UBANGIJI Allah, kamar yadda zuciyar babansa Dawuda ya yi.



**Yayinda Solomon ya bata zarafinsa na yi wa Allah biyayya, daya daga offisoshinsa mai suna Yerobowam ya sami wahayi wanda bai yi zato ba.**



**Wani annabi ya gaya masa cewa Allah zai raba mulkin Solomon zuwa kashi biyu kuma Yerobowam zai yi mulki a kan dangogi goma daga dangogi goma sha biyu na Isra'ila. Da sauri-sauri Yerobowam ya gudu zuwa Masar. Ya sani Solomon zai kashe shi in ya tsaya.**





**A karshe Solomon ya mutu. Dansa, Rehobowam, ya sa mutane suka biya haraji fiye da yadda babansa Solomon ya yi. Dangogi goma suka yi tawaye – suka zaba Yerobowam ya zama shugabansu. Babbar mulkin Solomon ya rabu kashi biyu, daidai kamar yadda annabi ya ce. Allah ba zai albarkaci rashin biyayya ba!**

# Sarki Solomon Mai Hikima

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**1 Sarakuna 1-12**

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

22

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**